**EPISODE 3**

**Characters**

*Laraba*

*Mai-Ungwa*

*Danjuma*

*Hannah*

*Jummai*

*Hassan*

---

**Episode 3, Scene 1**

***Northern Kaduna. Mai Unguwa's Compound. Afternoon.***

1. **MUSIC**: **THEME MUSIC**
2. **SFX**: **SOUND OF ROAD TRAFFIC WITH VEHICLE HORNS**
3. **SFX: INDISTINCT CHATTERS IN THE BACKGROUND**.
4. **MAI- UNGUWA**: Ina sauraronki 'ya ta. Kika ce ke wacece?
5. **LARABA**: Na'am Mai Ungwar, yi ha*k*uri, sunana Laraba Ibrahim, ni nas ce a *k*aramar asibitin garin nan.
6. **MAI- UNGUWA**: Toh! Yayi. Toh Nas Laraba, maraba da zuwa.
7. **LARABA**: Na gode Yalla*b*ai.
8. **MAI-UNGUWA:** Ina fatan cewa a matsayinki na sabuwar nas, kina da wata ingatacciyar shiri ma wannan garin?
9. **LARABA:** Ina da niyyar inganta lafiyar jikin matan garin nan ta hanyar basu shawarwari game da amfanin yin tazzara, domin rage yawan mutuwa da matsalolin da mata kan fuskanta.

10.**MAI-UNGUWA**: *Alhamdulillah!* Wannan na da kyau sosai. Zan baki goyon baya har zuwa *k*arshe. Mu ma mazan na bu*k*atan wannan ilimin domin mu kula da matanmu da kyau.

11.**LARABA**: Haka yake. Na gode Yalla*b*ai.

12.**MAI-UNGUWA:** Ina fatan kin fara sabawa da garinmu. Kina iya zuwa wuri na a duk lokacin da kike da wata bu*k*ata.

13.**LARABA:** Na gode Yalla*b*ai. **(PAUSE)** Um Mai Ungwar, ina dai neman wajen zama domin akwai wani a *d*akin dake cikin asibitin.

14.**MAI-UNGUWA:** Toh Laraba, wace irin gida kike so?

15.**LARABA**: Aah! Ba wani babban abu nake nema ba Mai Ungwa. Ina bu*k*atan *d*aki ne kawai, in da so, a cikin gidan wasu magidanta domin bani da aure.

16.**MAI-UNGUWA**: Wannan ba matsala bane. Bari na yi magana da wani sai na gaya miki, *In Sha Allah*.

17.**LARABA:** Toh, Na gode Yalla*b*ai. Ina matu*k*ar godiya da wannan taimako da ka bani.

18.**MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**Episode 3, Scene 2**

***Southern Kaduna. Hannah and Danjuma's Residence. Evening.***

**19. SFX:** **SOUND OF PLATES AND SPOONS DROPPED ON THE DINING TABLE. SOUND OF DOOR OPEN AND CLOSE. FOOTSTEPS APPROACHING HANNAH.**

20. **DANJUMA:** A'ah! Hannah na, me kike shirya mana yau?

**21. HANNAH:** Ah Danjuma, maigida na, abincin da ka fi so ne.

22. **DANJUMA:** **(HAPPILY)** Lalle! Ta yaya na ci sa'an samun ki a matsayin matata? Kin cancanci na rungume ki. Taho nan...

**23. SFX:** **<u>SOUND OF FEET SHUFFLING CLOSE TO EACH OTHER AS DANJUMA AND HANNAH HUG.</u>**

24. **HANNAH:** Toh zauna mu ci abincin kafin yayi sanyi.

25. **DANJUMA:** **(LAUGHING)** Toh Madam!

**26. SFX:** **<u>SOUND OF CHAIRS BEING DRAWN AS THEY SIT.</u>**

**27. DANJUMA:** Ki gaya mun, akwai labara ne?

**28. HANNAH:** Lafiya. Laraba ta kira, ta ce mini wai ta iso Kaduna. Wai zata ziyarce mu nan ba da da*d*ewa ba.

29. **DANJUMA:** Wato *k*awarki ta dawo nan da zama? **(TEASING)** Shi ya sa kike ta murmushi tun da na shigo gida.

30. **HANNAH:** **(DEFENSIVELY)** Haba Danjuma! Ina murmushi ne domin ka dawo daidai lokacin da na gama girka maka abinci. Shi kenan.

**31. DANJUMA:** **(TEASING MORE)** Kin tabbata? **(SERIOUS)** Amma dai kin san wasa nake dake. Ina ganin sabon shigan zai yi wa Laraba kyau. Zai taimaka ta manta da rashin saurayinta Jallo.

32. **HANNAH:** **(AGREES)** *K*warai da gaske. Ni kuma ina nan domin na kula da ita sosai...

33. **DANJUMA:** Kuma ma yanzu da muka dakata da tazzaran da muke yi, zuwanta zai taimaka mana da zaran kin *d*auki juna biyu.

34. **HANNAH:** **(LAUGHS SHYLY)** Kana da gaskiya Danjuma. **(PAUSE)** Kafin na manta, Mama ta zo *d*azu, ta ce na gaishe ka.

35. **DANJUMA:** Mama Kande, mahaifiyar ki? Yayi kyau da ta ziyarce mu.

**36. HANNAH:** Haka ne. kuma fa… Danjuma, tana tambaya ko 'yar uwata Tina na iya yin koyar aikinta, wato internship nata a ofishinka.

**37. DANJUMA:** **(CONFUSED)** Tina!? Wace 'yar uwarki ne Tina kuma?

**38. HANNAH:** 'Yar uwata ce ta nesa**.** Bama kusa sosai, shi yasa baza ka san ta ba, Danjuma**.**

**39. DANJUMA:** **(THOUGHTFUL)** Ehnn. Toh, meh take karantawa?

**40. HANNAH:** Ban da tabbaci, amma ina ganin Mama ta ce wai ko bizines ne, ko wani abu haka.

41. **DANJUMA:** Toh babu damuwa. Tun da ba aikin dindindin bane ba, zamu samo mata wani abu ta yi.

**42. HANNAH:** **(HAPPY)** Ooooh, na gode masoyi na. Amma kuma ka san cewa gidan Mama na da nisa daga nan**.**

**43. DANJUMA:** Na sani Hannah.

**44. HANNAH:** Saboda haka, ina tunani ko zata zauna tare da mu tunda mu bamu da nesa da ofishinka. Ko yaya ka ce?

**45. DANJUMA:** Ni? Bani da wata matsala da wannan, tunda dai kin amince da haka.

46. **HANNAH:** **(HAPPILY)** Na gode sosai masoyi na Danjuma.

**47. DANJUMA:** **(SMILING)** Menene bazan yi miki ba darlin na Hannah.

**48. MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**Episode 3, Scene 3**

**Northern Kaduna. Jummai and Hassan's bedroom. Late evening.**

**49. SFX:** **SOUND OF BED SQUEAKING AS SOMEONE SITS DOWN ON IT.**

50. **JUMMAI:** **(GIGGLING)** Kai! Hassan ke nan. Ka cika wasa *wallahi.*

**51. HASSAN:** **(LAUGHING)** Idan ban tsokana matata ba Jummai, wa zai yi?

52.**JUMMAI:** **(TEASING)** Ina jin ka Hassan. Duk da tsufarka?

53.**HASSAN:** Ni, tsoho? Haba Jummai, kin san ina nan da *k*uruciya na, da kuzari.

**54.JUMMAI:** **(GIGGLING)** Wa ke maganan kuzari? Kana da yara biyu, Jamil da Zarah. Toh ba za'a kira ka yaro ba kuma.

55.**HASSAN:** Manta da wannan. Barni na ji da*d*in rayuwata tare da iyali na. **(PAUSES, WHISPERS)** Ina yaran suke Jummai?

56.**JUMMAI:** Suna *d*akin Inna suna wasa, maigida na.

57.**HASSAN:** **(RELIEVED, ROMANTICALLY)** Ehen, yanzu zan samu lokaci tare da kyakkyawar matata.

**58.JUMMAI:** **(GIGGLING)** Ah, Hassan! Da yadda kake ta yi kwanakin nan, na gode ina kan aluran tazzara! In ba haka ba, da ba zan san abun da zai faru ba yanzu.

**59.HASSAN:** Shi ya sa hankali na kwance Jummai, in ba haka ba da bazan sake jiki kamar haka dake ba. Ina dai fata aluran basu baki wata damuwa ko?

**60.JUMMAI:** Ina nan lafiya. Ina dai tunanin canzawa zuwa wata hanyan tazzara mai da*d*ewa**.**

**61.HASSAN:** **(CURIOUS)** Meyasa? Na *d*auka kin ce baki da damuwa da wannan hanyan?

62.**JUMMAI:** Haka ne. Amma Hassan, ka san mun yarda cewa zamu *d*an dakata ma wasu shekaru kafin mu samu wata haihuwa.

63.**HASSAN:** Eh.

64.**JUMMAI:** Toh, ni na gaji da zuwa asibiti bayan kowanne wata biyu domin kar*b*an alura.

**65.HASSAN:** Shi kenan Jummai. Na gane kuma na yarda. Kin san hanyan tazzaran da zaki so komawa kai?

66.**JUMMAI:** Ina tunanin robar hannu/ashanan mata, wato implant kenan.

67.**HASSAN:** Wannan da ake sakawa a hannu, wanda ke kaiwa kamar tsawon shekara uku ko biyar ko?

68.**JUMMAI:** Eh, shine. Amma ina tunanin zai fi dacewa idan mun je asibiti don mu samu shawara.

**69.HASSAN:** Tabbas. Na amince da haka. Ina godiyan cewa muna amfani da tazzaran haihuwa. Kalli yadda ke da yaran kuke cikin *k*oshin lafiya.

70.**JUMMAI:** Haka ne fa. Na gode wa Allah, kuma ina maka godiya da ka nuna ganewa da goyon bayanka Hassan.

**71.HASSAN:** Kula da ke da yara na ha*kk*in dake rataye a wuyana ne, ba sai kin yi mini wata godiya ba. Mu dai yi wa Allah godiya da Ya bamu ganewa da ha*d*in kai.

**72.JUMMAI:** Ha*k*i*k*a.

**73.HASSAN:** Toh Jummai, ba da da*d*ewa ba zamu je asibiti mu ga jarumin aikin tazzaran haihuwa domin mu samu cikakken bayani.

**74.MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**Episode 3, Scene 4**

**Southern Kaduna. Hannah and Danjuma's residence. Afternoon.**

75. **SFX:** **<u>HAUSA MUSIC PLAYING ON A STEREO IN THE BACKGROUND.</u>**

76.**HANNAH:** **(EXCITED)** Kai Laraba! Ina farin cikin zuwanki nan. Da kin ga yadda nake ta rawa a cikin gida ni ka*d*ai da kika gaya mun an mai da ke Kaduna.

**77.LARABA:** Hmm Hannah, ai sai da na *d*an ta*b*a. Mafi damuwa shi ne da mutane suka fara maganganu cewa ina amfani da rashin sa'a na ina ta kashe duk samarin da suka neme ni da aure, harda Jallo ma.

**78.HANNAH:** **(ANGER)** Haba! Wace irin banzan magana ne wannan?! Meyasa mutane ke da mugunta haka? Bayan duk wahalan da kika sha?!!

79.**LARABA:** Amma Hannah, ai ba laifin su bane. Ke ma zaki shaida cewa ina da rashin sa'a sosai ma domin duk wanda na so yana mutuwa kafin lokacinsa.

**80.HANNAH:** **(SADLY)** Laraba kar ki yi irin wannan magana. Ba laifin ki bane.

81.**LARABA:** Baki sani bane Hannah, har ya kai ga mutane na *k*in zuwa asibiti a dalili na.

82.**HANNAH:** **(SHOCKED)** A'aah!

83.**LARABA:** **(CUTS IN)** Kuma wanda suka yin *k*o*k*arin zuwa na *k*in na ta*b*a su, ko na basu kulawa domin tsoran zan kashe su suma.

**84.HANNAH:** **(SADLY)** Kai! Wannan ba da*d*i. Kin ta*b*a fa. Ina ganin wannan sabuwar yanayi a nan zai taimaka miki Laraba.

**85.LARABA:** Ina murna da na tafi, in ba haka ba da na haukace wata rana, saboda takaici …

| | |
|---|---|
| **86.HANNAH:** | **(CUTS IN)** A ina? Allah Ya sauwa*k*a! **(GLADLY)** Ina dai jin da*d*in zamu ringa ganin juna … **(TEASING)** kafin dai ki yi aure! |
| **87.LARABA:** | **(SMILING)** Hannah, kin san ban dawo nan ba don na yi aure. |
| **88.HANNAH:** | **(LAUGHING)** *K*ila ba nufinki bane, amma ba zaki *k*i ba idan kin samu, ko ba haka ba? |
| **89.LARABA:** | Kin ga Hannah, ban da niyyar aure har abada. Bayan mutuwar Jallo ina ganin cewa aure ba rabo na bane. |
| **90.HANNAH:** | **(PROMISING)** Kar ki damu Laraba, zaki samu miji nagari wanda zai canza miki tunani. |
| **91.MUSIC:** | **<u>THEME MUSIC</u>** |